Ku kula da sallah da abinda hannayenku suka mallaka

Daga Anas - Allah Ya yarda da shi ya ce: Wasiyyar Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - mai gamewa ta kasance lokacin da rasuwarsa ta zo masa: «Ku kula da sallah da abinda hannayenku suka mallaka, ku kula da sallah da abinda hannayenku suka mallaka», har Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya fara gargarar mutuwa, amma harshensa bai iya faɗinta ba.

[Ingantacce ne] [Nasa'i ne ya ruwaito shi cikin Alkubra da Ibnu Majah]

Mafi yawan wasiyyar Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ga al'ummarsa ta kasance alhali shi yana cikin magagin mutuwa: Ku lazimci sallah ku kiyayeta, kada ku rafkana daga gareta, haka nan haƙƙoƙin abinda hannayenku suka mallaka na bayi maza da kuyangi mata ku kyautata mallakinsu, bai gushe ba yana maimaita ta, har maƙogwaransa ya fara gargarar mutuwa da ita, harshensa bai kusa ya bayyananar da ita ba.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66359